



# Rai Madawwami, A Yalwace

*Yesu ya mutu da mutuwarmu domin mu sami ran Sa*



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Yesu ya kira kansa "makiyayi mai kyau" (Yahaya 10:11, 14). Za a iya takaita tanadin makiyayi, kamar yadda aka nuna a Zabura ta 23, a cikin kalma ɗaya mai girman gaske: cikakken tsaro. Amma ku tuna cewa ana ba da dukan tanaje-tanajen gwargwadon miƙa kanmu ne. Idan miƙa kanmu cikakke ne, tsaronmu ma cikakke ne. Idan akwai karanci na miƙa kai, to, ba za mu iya samun cikakken tsaron da Yesu yake bayarwa ba.

Za mu iya ƙarfafa wannan misali na Tsohon Alkawari ta hanyar duban kalmomin Yesu a cikin Sabon Alkawari:

> "Ɓarawo yakan zo ne kawai don sata, da kisa, da hallakarwa. Ni kuwa na zo ne domin su sami rai, su kuma same shi a yalwace" (Yahaya 10:10)

Yesu yana gaya mana dalilin da ya sa ya zo cikin duniya. Ya taƙaita shi da wata kalma mai sauki: cewa "za mu sami rai." Ba rai ɗan kaɗan ko taƙaitacce ba, amma rayuwa "yalwatacciya." Rai mai yalwa. Rai ga kowane fanni na rayuwarmu. Rai da zai wadaci kowane ƙalubale da kowacce damuwar da ke gabanmu.

Bayan haka, a gaba kaɗan, Yesu ya yi amfani da kalmar nan, “rai madawwami”:

> "Tumakin nan nawa sukan saurari muryata, na san su, suna kuma bi na; ina ba su rai madawwami, ba kuwa za su hallaka ba har abada; ba kuma mai ƙwace su daga hannuna." (Yahaya 10:27–28)


Lura da ƙwayar maganar: "Ina ba su rai madawwami, ba za su hallaka ba." Bisa ga wannan ayar, mun ga cewa Yesu ya zo ne domin mu sami rai madawwami, ran da ya zarce wannan duniyar. Ran da ya zarce kabari. Ran da ya ke madawwami. Na taba jin wani ya yi wannan sharhi mai zurfi: "Na gaskata cewa zan rayu tare da Allah domin Allah

ya zama raina." Wannan shi ne irin ran da Yesu ya zo ya ba mu - na har abada.

Na gode maka, Yesu, saboda aikin ka a kan gicciye. Ta wurin mutuwarka, ina da rai madawwami a yalwace, domin Yesu ya mutu da mutuwata domin in sami ransa. Amin.

**Abincin Yini** ★

Kwafi: WD-B097-118-HAU
Sabuntawa ta karshe: 09 Sept 2026
Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources




© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.